*Bijochs Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2- 017 (Pg. 187-197)*

# FARFESA: Ɗalibin Ɗalibai, Malamin da Malamai Ka Buƙata (Nazari Cikin Falsafar Bahaushen Adabin Waƙoƙin Baka)

**Aliyu Muhammadu Bunza**
(Farfesan Al'adun Hausawa)
Sashen Koyar a Harsunan Nijeriya
Jam'ar Jihar Sakkwato

Takardar da aka gabatar a taron walimar Farfesa Mu'azu Sa'adu Kudan a Harabar Makarantar Firamare ta garin Kudan, Ƙaramar Hukumar Kudan, Jihar Kaduna, Nijeriya, ranar Lahadi 4 ga watan Janairu 2026, ƙarƙashin Shugabancin Hon. Isa Muhammad Ashiru Sarkin Bai Zazzau, tare da haɗin kai na Ƙungiyar Taimakon Marayu da Ƙungiyar Matasa ta Garin Kudan (KYDI).

**Gabatarwa**

Ilimin boko baƙon ilmi ne a ƙasar Hausa wanda ilimin addinin Musulunci ya riga shi shiga da kafuwa da barbazuwa. Da yake addinin Musulunci ba da yaƙe-yaƙe da rigingimu ya shigo ƙasar Hausa ba ya samu maraba babba daga Hausawa. A tarihance shigar kalmar Shahada ƙasar Hausa babu tabbacin kwanan wata sai dai kwatance-kwatance na shigowar Larabawa 'yan kasuwa, saduwa da daular Borno, haɗuwa da fadar Adar, shigowar Misirawa da Kibɗawa ga su nan dai. Haka ma shigowar ilmin boko na ga nason cinikin bayi, gangarowar Mishon, kasuwanci da Mulkin Mallaka. Duk waɗannan abubuwa za a ga hanyoyi biyu za su kasance na bazuwar ilmin karatu da rubutu a ƙasar Hausa, wato addinin Musulunci da addinin Mishon. Tushen kalmar "Farfesa" ga addinin Mishon ya fito wanda ya girkar da ilmin boko bayan rusar da gwamnatin Musulunci ta ƙasar Hausa.

**Dabarun Bincike**

Taken wannan takarda ya nuna wani sabon abu ne ake son a leƙo. Da yake tushen kalmar daga Ingilishi yake ko Faransanci dole a leƙo ƙamusun harsunan da ke fitattu a harsunan. Wallafe-wallafen da aka yi na littattafan girmama Farfesoshinmu musamman wanda aka yi wa Farfesan Hausa da kuma Farfesoshi da ke Hausawa ko da ba a fannin Hausa suka yi ayyuka za su taimaki wannan takarda. Farfajiyar intanet ta agaza sosai. Ayyukan da aka yi fannonin ilmi da ilmin Falsafa da Adabi da Harshe da Al'adu na kowane fanni za su agaza. Nazarin ya leƙo waƙoƙin baka da yawa da aka ga goyon bayansu ga ƙudurin da ake so a kafa a faɗaɗa bayaninsa. Hira da masana da ɗalibai da mawaƙan baka da rubutattu ya taimaka sosai. Saduwa da Farfesoshin Hausa da waya da ga-ni-ga-ka ya taimake ni wajen isar da wannan saƙo sosai.

### Fashin Baƙin Taken Takarda

Malamanmu sun yarda a yi amfani da kalmar "Farfesa" wajen fassara kalmar "Professor" a Hausa. Dalilina ke nan na saka ta a goshin takarda. Kalmar "Ɗalibi" ararriya ce daga Larabci amma a yau ta zama karɓaɓɓiya a fagen nazarin Hausa. Haka kuma, kalmar "Malami" ko "Malam" duka ga Larabci aka aro su yau sun zaunu a cikin nazarce-nazarcen malamai da ɗaliban Hausa. Manunin taken dai shi ne, duk wanda aka kira da sunan "Farfesa", to an tabbatar da ya fara koyo tun karatun Firamare zuwa Jami'a da zai samu manyan digirorin jami'a ya zuwa ranar da ya samu sunan a hukumance.

### Ra'in Bincike

Ɗora bincike a kan wani ra'i na masanan falsafa magabata ba laifi ba ne, haka ma aka saba. A ɗan nawa hange a yi amfani da ra'o'in gargajiya ga mutanen gargajiya da abin ya shafa zai fi fito da hoton abin a kan madogarar harshensu da adabinsu da al'adunsu. Na tuna makusanciyar takarda irin wannan da na gabatar kan wani malamina Farfesa Abdullahi Bayaro Yahya na Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato, an ɗora ta a kan karin magana: "Sannnu ba ta hana zuwa sai dai a daɗe ba a kai ba", sai na sauya mata awo da "Ko za a daɗe ba a kai ba". To, ko wannan na ɗora ta kan babban adabinmu karin magana mai cewa; Gani ya kori ji" wato in ka ji labarin wane ne Farfesa ba ka gan shi ba, ga wani a fili ka gan shi domin kore laburan Farfesoshin da ka ke ji ba ka ga kowa ba. In ko ka taɓa ganin su bayan ka ji labarin wasunsu, to yau za ka ji labarin yadda suke da yadda karatunsu na ilimi ke son su zama. Na gayyato makaɗanmu na baka domin su jagoranci iƙirarin "gani ya kori ji".

### Wane ne Farfesa?

Fashin baƙin wannan kalma zai fito da dalilan yin wannan takarda domin samun goyon bayan masu saurare da masu karatu da samun gyare-gyarensu. A fassarar Kamusun Intanet sun ce:

Ingilishi:

> *A Professor is an expert educator at a College or University holding the highest academic rank, responsible for teaching, conducting research, developing curriculum, and mentoring students, often requiring advanced degree (like a PhD) and significant scholarly contributions; the terms specific application (e.g., highest rank vs. general University teacher) varies by country, notes.*
>
> *Ingilishi:*
>
> Farfesa ƙwararren ma'ilmaci ne a babbar makaranta da Jami'a wanda yake da darajar

ilmi babba maɗaukakiya (kan kowa). Farfesa zai kasance ɗaukar nauyin koyarwa, jagorantar bincike da ƙago dokokin koyarwa da jagorantar ɗalibai mabuƙatun babban digirin PhD, kuma ya zama mai bayar da gudunmuwa babba a fagen ilmi manyan kalmomi da aka yi amfani da su na darajar ilmi babba da cewa malamin jami'a ya bambanta daga wata ƙasa da wata.

A fassarar Wikipedia https://en.wikipedia.org sun ce Kalmar "Farfesa" Ingilishi ya aro ta daga harshen "Latin" a wajensu yana nufin "mutum ƙwararre" don haka aka ƙara da cewa: Farfesoshi mutane ne za a same su ƙwararrun masana a fagen iliminsu su kasance malamai masu babbar daraja ta ƙoli.

Waɗannan ma'anonin da aka bayar na tabbatar da gaskiyar daraja/girman da makarantu/Jami'o'in Nijeriya ke bai wa malami na zama "Farfesa", su ne ya kasance ya yi karatun Firamare lafiya ya ci jarrabawarsa. Ya kasance ya shiga makarantar gaba da Firamare ya kuma ci jarrabawar ƙarewa. Ya samu digiri a yarjajjiyar Jami'a, digirin ya kasance mai sakamakon daraja. A al'adance, ana son yana da digirin M.A. M.Sc. da digirin Ph.D. An so ya ba da gudunmuwa ga koyarwa a Jami'a da duba ɗaliban ƙaramin digiri da manyan digiri da rubuce-rubuce da wallafe-wallafe masu cika hannu daga shekarar da ya karɓi digirin PhD zuwa shekaru (10) kafin a ɗora shi ga kujerar "Farfesa".

Kasashe da dama suna da hanyoyin bayar da kujerar bisa ga yadda suka kalli ilmin boko. A duniyar ilmin boko idan ilmi ya tabbata ilmi ya gagari tuƙewa ga kowa babu abin da za a yi wa ma'abocinsa kyauta da shi sai muƙamin Farfesa. A ƙasar Indiya – Soborno Isacc Bari ɗan ƙasar Bangaladesh mazauni Amurka an ba shi kujerar yana ɗan shekara bakwai (7). A ƙasar Pakistan Alia Sabur ɗan shekara goma sha tara (19) ya samu kujerar a Guiness World Record, kasancewarsa mai ƙaranci shekaru a duniyar zamaninsa (2008) a Jami'ar Konkut. Haka a Amurka Shania Muhammad ya zama malami mai qarancin shekaru a duniyar lokacinsa ɗan shekaru goma sha shida (16). A Nijeriyarmu, Chinanye Egbo shi ne malamin Jami'a na farko mai ƙarancin shekaru (24) saboda kasancewarsa da basira wadda babu kamarta a Afirka. A taƙaice, dokar zama Farfesa ga shekaru babu ita a duniyar zamaninmu. Babbar buƙata ita ce a samu mutum haziƙi da duniya babu kamarsa kuma hazaƙar ilmin ba ta da abokin jayayya ko ga injin mai ƙwaƙwalwa (computer). A yau (2025) bincike ya tabbatar da cewa farfesa da ya fi kowane farfesa yawan shekaru a duniya ita ce Chilukuri Santhamma 'yar ƙasar Indiya a Jami'ar Centurion a Andhra Pradesh, tana da shekaru (93). A Nijeriyarmu farfesan da ke da yawan shekaru a duniya shi ne Kenneth Dike a Jami'ar Ibadan a shekarar 1956 (1917-1983). A tarihance daga shekarar 2024-2025 muna da farfesa dubu

goma da ɗari biyar (10,500). Bisa ga wannan ɗan hange za mu ce, a Nijeriyarmu Farfesa shi ne: Mutum ko ɗan boko da ya kai ƙolin ƙoli yana bokon da ya karanta. Fitacce cikin masanan Jami'a da ya cancanci wakiltar fannin ƙwarewarsa mai ilmin da ma'ilmanta suke ilmantar a kira shi malam ya cewa malam "Malam" a baya a ɗalibansa a gaba da shi malamansa, hannun dama matambaya fatawowi, hannun hagu masu gardama da son jayayya.

## Ɗalibin Ɗalibai

Ga ɗan bayanin da ya gabata, babu Farfesan da ba ga wani ya samo fasahar da ya shahara ba. A ƙasarmu dole sai an yi karatu matakai-matakai, kowane mataki da malamansu da za su koyar da shi, su ne malamansa da wasu malamai suka koyar. Dalilina ke nan na ganin Farfesa "ɗalibi" kuma "ɗalibin ɗalibbai". Mu ɗan waiga baya mu ga tsarin addibbanmu na gargajiya musamman mawaƙan baka, za a ga jagoran waƙa shi ne Farfesa 'yan karɓi su ne ɗalbansa alhali shi ma ya yi zama ɗan karɓi gabanin ya kasance uban kiɗa a yau. Makaɗa Dr. Ibrahim Narambaɗa ya tabbatar da haka a ɗan waƙarsa;

| | |
|---|---|
| :<br>: | Uban kiɗi Narambaɗa<br>Yau ga niga Kwatarkwashi |

Kowane makaɗi 'yan amshi su ne yaransa, shi ne malami su ne ɗalibai wasu sai ya mace su hau kujera, wasu tun yana raye su kafa tasu ƙungiya. Don haka nake so in yi amfani da saƙunan makaɗa domin fito da hoton Farfesa sosai da sosai kowa ya shaidi cewa ɗalibin ɗalibbai ne.

## Ladabi

Babbar lambar Farfesa ita ce samunsa mai ladabi cikin komai a rayuwarsa. Matuƙar ya bari girman kai da neman suna suka shige ga ilminsa, to bai yi wa ilmi adalci ba. Dubi irin ladabi da ya gudana a cikin tsakanin Dr. Ibrahim Narambaɗa Tubali da yaransa. Shi da kansa ya kira su "yarana" ya ce:

| | |
|---|---|
| Jagora:<br>:<br>:Yara:<br>:<br>:<br>:<br>Gindi: | Ku yarana na tambaye ku;<br>Shin kowag ga wuta<br>An ka ce a ɗebo wa ka zuwa?<br>Wanda yag gani ka zuwa<br>In bai je ba yai batun banza<br>Ko can dauri dai batun banza<br>Daɗin hwaɗi garai<br>Ya ci maza yak wan shi na tsare |

Dubi ladabin da Uban Waƙa ya yi ga yaransa (ɗalibansa), dubi irin amsar da suka bayar cikin ladabi kowanensu bai yi rashin kunyar da bai bari a ji amsarsa ba.

## Kanƙantar da Kai ga Ilminsa

Yana da kyau Farfesa ya san baiwar da Allah Ya yi masa ba ta girman kai da bugun gaba da amsa kiran suna ana doro ana bugun gaba. Farfesa baiwar Allah ce mai nuna mai darajar mai ƙasƙantar da kansa ga wanda ya ba shi girman ne, ba shi ya ƙwato da ƙarfi ba. In an ce ya yi kure ya yarda, wa ya wuce kure? Waye ba a yi wa gyara? Ku dubi

yadda fitaccen mawaƙan ɓarayi ke gaya wa mutanen da ke yi masa mugun zato na halaka ranar gamonsa ga MahaliccinSa kai tsaya ya ba da amsar

ƙasƙantar da kai ga Allah, ya saukar da murya ƙasa ya ce:

:Kwaz zaka bangon duniyar ga
:Yay yi bakwai biyu ya yi saɓo
:Sai in bai da idanu bai da baki
:Sai dai rahamar Allah in Yanai muna
:Alhaji Gambo mai Kalangu
:Ba don wani aiki mai yawa ba.

Farfesa ya san da baiwar da aka yi masa dole tana da mahasada ko daga cikin abokansa Farfesoshi da ba su kai shi suna ba, da waɗanda ke ganin ya hana a ji su, da dabirtattun malamai da ɗalibai. Don haka makaɗa Gambo ya ce kowa mai saɓo ne in ya sani in bai sani ba, wanda ba ya da idon gani da bakin magana kawai ke tsira ranar hisabi in ji shi. Yarda da Gyara Ba Musu Ba Ne, Ilmi Ne Ɗaukakar da Allah Ya yi wa Farfesa ya san da cewa tuna ɗalibtakansa ce ta fara ba wahayi aka yi masa ba. Daga gyare-gyaren kurakurai da ake karo da su a ɗalibta da malanta aka kai kujerar karɓar gyara da gyara kure. Da yawa za ka zo da magana mai hujja, wata hujja ta fi taka ƙarfi, yarda da su biyun shi ne Farfesa kamar yadda muƙabilar Makaɗa Walga Bunza ya yi da yaransa kai tsaye ya gaya musu:

Jagora: Da duniya da Lahira duk ɗai.

Sai yaran suka gaya masa:

| | | |
|---|---|---|
| Gindi: | Sha kiɗinka Walga mai turu<br>Walga ƙanen Magaji duniya daɗi. | : |

| | | |
|---|---|---|
| Yara: | Ko wak kwan ta dama Bai ji daɗi ba. | : |

Da ya dubo su fusace suka gaya masa:

A ganin Walga da duniya da lahira mutane iri biyu ne da masu samu da marasa. A duniya akwai attajirai akwai talakawa a lahira akwai 'yan Aljanna akwai 'yan wuta. A ganin wani mawaƙin tashe na ƙasar Gwandu a Karamar Hukumar Bunza a wani gari mai suna Yarma, da ya ga wani mawaƙin tashe cikin garin Bunza ya fi shi makaɗa masu daɗin kiɗi, sai ya ba yaransa haƙuri ya gaya wa masu sauraro cewa:

| | |
|---|---|
| Jagora;<br>Yara:<br>Gindi:<br>: | Sai dai a fi mu Kalangu da Kurkutu<br>Amma ba a fin mu daɗin baki<br>Yau da borin goje<br>Kana da borin tashe |

A gaskiya ya fi su iya waƙa, su ko sun fi shi makaɗan gado. Ai makaɗa Gambo ya san makaɗa Kassu Zurmi

maigidansa ne a waƙar ɓarayi koyaushe yakan ce:

| | |
|---|---|
| Jagora: : | Maigida Kassu na waƙar ɓarayi<br>Allah Ya ji ƙainai kan da in zo |

Ya san Kassu Zurmi ya fi shi kiɗin ɓarayi mai shiga rai amma bai fi ambaton sunan ɓarayin ba, don haka yake cewa:

| | |
|---|---|
| Jagora ; : : | Ko an fi ni kiɗin waƙar ɓarayi<br>Ba a faɗin sunan ɓarayi<br>Kamar yadda Gambo ke faɗinsu. |

Farfesa duk wani ilmi gare ka cikinsa akwai wanda ya fi ka sanin wani abu daga ciki durƙusa ka zama ɗalibinsa ka san abin da ba ka sani ba domin kirarinka "ɗalibin ɗalibbai", to ka bi ɗalibai ka koma Mallam dole malamai suce maka "Shehi".

**Kujerar Farfesa ta Koyon Karatu Ce**

Yana da kyau malamanmu su sani cewa, da an ce maka Farfesa to lokacin ka hau kujerar koyon karatu domin karatunka ya tabbata karatu masu karatu sun tabbata ba a sauke karatu har mutuwa. Don haka da Farfesa ya aje karatu da bincike da rubuce-rubuce, to ya sauka kujerar nan ke nan ya zauna gida ya sa wa masu yi ido. A lokacin da makaɗa Gambo ya yi nisa cikin waƙar ɓarayi ana ganin babu wani sai shi, a gaban mutane ya ce; duk ɓarawon hatsin gona (damma) ba ya son sa, domin ya san satar dame ta ɓarayin banza ce da ba su cancanci a yi musu waƙa ba.

Kai tsaye yace:

: "Ɓarawon damma ba ni so nai".

Tun da ba ya son sa batun a yi masa waƙa ba ta taso ba. Shi ya san sata, ya san ɓarayi, don haka ya cire shi daga ɓarayin gaske. Can ya sake cewa:

: Amma ku tsaya in hidda Hantci".

To, ka ce ba a son ɓarayin damma domin a matsayinka na masani ɓarayi ka san ba kowa ba ne, sai ya ce dalilin tubana shi ne:

Jagora: Ko ba shi da yuƙa bai da Lauje

:Ko da guda yar ratci Jenna

:Wallahi ana ɗaurin tamanin

A duk rayuwar kiɗin sata na Gambo babu ɓarawon da ya kai "Hantci" asirin sata da ƙarfin hali domin da ya je garinsu "Hantci" Karamar Hukumar Suru, Jihar Kabi sunan garin Hore, yana kiɗa an koro Hantci da dare da dami akan sa yace:

:"Hantci shi jefa, su su jefe shi

:Har aka zo hilin kiɗinmu".

Daga wannan lokaci Gambo ya gane duk ficen da ya yi na waƙar ɓarayi da zama da su bai san komai ba sai wajen Hantci. Duk Farfesan da ya kula da wannan hirar Gambo ya san zaman Farfesan kowane fanni hawa kujerar koyo

ce, koyo ko ba a gama shi sai an mutu. Basarake Cikin Sarakuna Ya Bar Alfahari. A tarihin ɗan Adam ilmi ya haifar da Sarauta domin kowane ya san ilmin da aka kafa ƙasarsu ko garinsu shi ya ba shi Sarautar mazauninta. Farfesa ya san da cewa, komai yawansu a jami'a da fannonin da suke koyarwa za a tarar da halayya da ɗabi'u dole wani ya fi wani gwargwadon awon da mutane ke yi musu. Mu nazarci wannan saƙon makaɗa Musa Ɗanƙwairo da yace:

Jagora: Dogon Sarki yana da kyawo

| | |
|---|---|
| Yara: | Ranar da an ka je Daba :Ya yi kyau da riguna |
| Jagora: | Shi wanga ɗan gajere :Ku aje shi gun rabon dawo |

| | |
|---|---|
| Yara: | Shi kai ma wanga dunƙule :Shi kai ma wanga dunƙule |

Jagora: In dai wurin akwai mata

Yara: Hat tuman gara shikai

| | |
|---|---|
| Gindi: | Ya riƙa da gaskiya Muhammaduu Muhammadu :Karsanin gidan Maisaje shirinka ya yi kyau. |

Dole mu san da cewa kujerar Farfesa ba ta alfahari ba ce, ba ta fasiƙanci da cin amanar ɗalibai da malamai ba ce. Ka da mu yi mamakin ƙila duk Sarakunan dogaye ne amma aka mayar da ɗayan gajere domin a rataya masa rigar fasicci. Matuƙar Farfesa ya tsare mutuncin kujerarsa da amana dogon mutum ne ko da a halicce Wada Allah Ya halicce shi.

**Dangantakar Ɗalibbai, Malamai, Farfesoshi da Farfesa**

Duk wanda aka ce wa Farfesa ɗalibin wani ne kuma malamin wani ne, kuma Farfesan wasu Farfesoshi ne na tare da su a Sashensu ko tsangayarsu ko jami'arsu ko jami'o'insu. Ko a zaman jahilai dole a yi karo a matsalolin ƙiyayya da rashin jituwa da rashin yarda da son kai da giba da ɓannan sunan. Dole ma'ilmanta su san da cewa kujerar Farfesa kamar irin ta kowane irin mulki ne ba ta kasa kai ba, ba ta ƙin amfani juna da ƙasa ba, shi ya sa makaɗa Sani Aliyu Ɗandawo yace:

Jagora: Mutane mu bar jayayya

:Allah Shi Ka bai Ya bashi

:Mu zo mu rufa mai baya

:Akwai gaba na nan kuma

:Ba duka za a zama Sarki ba.

Yadda duk ake yi wa Farfesa taron walimar murna ya hau kujera, to ya kasance haɗin kansa da ɗalibansa da malamansa da abokan aikinsa da mazauna gidansu da unguwarsu da garinsu da ƙaramar hukumarsu da jiharsu da ƙasarsu. Haka ake yi a wayayyin ƙasashe sai a ga Farfesa ya kai shekaru (100) ana tare da shi yana bada gudunmuwarsa a fagen nazarinsa. Sa-in-sa ta Kasance ta Gudunmuwa Idan muka dubi wasan dambe da kokuwa da sharo na ƙoƙarin rinjayar

abokin gasa ce ba gudu ba gudunmuwa ga ‘yan kallo ba. Idan sa-in-sa ta haɗa Farfesa da wani Farfesa ko wasu a kula da yadda Raƙumi da Jaki suka yi sa-in-sa a fannin ilminsu domin a agaji ilmi ba a ruguza shi ba, Makaɗa Garba Maitandu Shinkafi a waƙar Jaki cewa ya yi:

| | |
|---|---|
| Jagora; | Raƙumin ya ce mai<br>:Jaki ƙasar ga ni ɗai ab ba a so |

| | |
|---|---|
| Yara: | Kullum sai an yi min aji<br>:In taso ina kuka |

Jagora: Jaki ya ce ma raƙumi

| | |
|---|---|
| Yara:<br>Yara: | Dan Allah raba mu<br>Ni don ganin wuyana<br>:Ab ba a ci na<br>:Kullum an ka yo aji |

Jagora: Ga kulkin bugawa
:In nat tuntsire da kaya
:Ba mai ije min su
:Da kwance sai a bi ni
:Ga hanci ana daga
Gindi: Sai na yi ma kiɗi Sarkin tuttular kaya
:In ana jida Jaki ba a tausai nai.

A taƙaice ayyukan Farfesa ba na jayayya ba ne ayyuka ne na bayyana abubuwan da ya gano domin ɗora su ga wasu domin samun ci gaba. Mu yi godiya ga Allah cikin Farfesoshi dubu goma da ɗari biyar (10,500) na Nijeriya ba mu ga fitattun ayyukansu na jayayya da juna ba, sai dai daɗa juna sani.

**Gurbin Farfesa a Duniyar Zamaninsa Malami da Makaranta**

Wanda duk ya hau kujerar Farfesa a duniyar zamaninsa shi ya kamata ya yi amfani da ilminsa ga mazauna zamaninsa. Yana da kyau ya kiyaye da sanin cewa a koyaushe ake neman shugaba ana iya tunkararsa domin ya yi amfani a kujerar da aka ɗora shi a kai.

Dubi yadda Dr. Narambaɗa ke cewa:

| | |
|---|---|
| Jagora: | Amadu dubi mazan gaba<br>:Dubi na baya |

| | |
|---|---|
| Yara: | Ka duba ba dama<br>:Ka duba hauni |

| | |
|---|---|
| Jagora: | Ka san da jama’ar ga<br>:Da an nan |

| | |
|---|---|
| Yara: | Kauye da birni<br>:Ba su da jigo sai kai |

Jagora: Maɗi bai kai ga zuma ba

| | |
|---|---|
| Yara: | Kowal lasa shi ka hwaɗi<br>:Kwandon wake bai kai ga damen gero ba |

Jagora: Ɗan akuya ko ya yi ƙaho

Yara: Ya san bai yi kaman rago ba

Jagora: Duk wada ɗan Sarki yad tunzura

Yara: Kar ku raba shi da bawan Sarki.

Da jin yadda Dr. Ibrahim Narambaɗa ke ba da waƙa 'yan amshi na karɓawa an san ba koyar da su ake yi ba. Karatu ake yi tare da neman ƙwarewa yau gobe a kafa makaranta. Farfesa ya lura, gaba da ɗaliba bai taso ba, bale jiye mishi da ƙoƙarin ɓata masa suna ai naka ne ke ɓaci ba nasa ba. Kai ko ɗalibi ka san komai ka zama koyar da kai aka yi.

**A Daina Faɗar "Na Iya" a ce, "Na Koya"**

Farfesa ka sani a gun ɗalibai malami kake, a gaban malamai kai ne malami, ka ɓoye wannan sirri a zuci ka riƙe kirarinka na ɗalibin ɗalibbai. Ga yadda Sani Ɗanbalɗo ya koyar da mu yadda za a yi gyaran kurakuran bugun gaba, ya ce:

Jagora: Kun san layun tsari gare ni

:Me al layun tsayinka Mamman?

:Dunƙullen dawo gami da nono

:Kowas sha su ba shi yin kasala
:In ko an yi gardama a dama

:Rabbana Allah Ka taimake mu

:Mu samu fitar kai cikin tukunya

Babban Shehunmu Sani Ɗanbalɗo ba ya da 'yan amshi/karɓi ga shi ya ɓaro ta ya ce yana da "layun tsari". Da ya ji tsoron a ɗan jarraba layun nasa, ya tambayi kansa layun. Cikin gaggawa ya goge na iya, ya kawo na koya da kowa zai iya yarda da shi ya fassara layun ya kuma faɗi "tsarin" da suke yi wa kowa. Ya san faɗin na iya zai haddasa gardama, ya cewa masu son a yi garama su tsaya a dama, a sha, in ciki ya cika a yi gardama in jiya. Da irin wannan salo Marigayi Garba Gwandu ya yi tamat ga gagarumar waƙarsa ta gasa da cewa:

Tammat kun ji ƙarshenta,

Haɗin kai kun ji sunanta,

Da an tambaiku way yi ta,

G.G. Gwandu yay yi ta,

Bayero yar rubuta.

(Garba Gwandu: 1982).

Wanda duk bai san Marigayi Garba Gwanu ba in ya ji wannan waƙar zai ce, mai karantawa ba shi ne G.G. Gwandu ba. Ga shi fitaccen Sha'iri amma cewa ya yi G.G. Gwandu kawai bugu da ƙari ya nuna wa mai saurare cewa shi fa ko rubutu bai iya ba (makaho) ne sai ya gaya muna marubucinta. Da ɗai Farfesa na ɓoye sunan kujerarsa maimakon Farfesa Mamman Shata Katsina ya ce Mamman Shata kawai ya bari ayyukansa su fito da sunansa ƙiri-ƙiri ga masu sauraronsa da masu karanta ayyukansa. Dubi ɗan damben da ya yi kirarin: "Yaronkai da Uwaka Uwa ku"Da aka kai ga bugu da haɓarsa ya faɗi jicce sai da aka tayar da shi,yace:"Kaddara Musulmi takaci, In ta faɗa Kafiri taikunya". Makaman Farfesa
A al'adance kowane basarake makamansa na kare kansa da kare jama'arsa su ne Sarakunan ƙasarsa da fadarsa. Shugaban ƙasa da gwamna

makaman tsare ƙasa da jiha suna ga Sojoji da 'Yan Sanda da Ministoci da Kwamshinoni, kowane Farfesa a duniyar yau da jiya ba ya da makamai da suka fi litattafai da mujallu da intanet da kafofin yaɗa labarai da tarukan ƙara wa juna sani. Wanda duk ke kan kujerar Farfesa yana da kyau ya kasance yana da ɗakin karatu na kansa da ya tara ayyukan abokin aikinsa da ayyukan kansa da kayan gudanar da bincike. Sunan Farfesa kawai ba ya ceto ƙasarmu da jihohinmu da ƙananan hukumominmu da garuruwanmu da gidajenmu da kawunanmu ga jahilcin zamaninmu. Farfesa ya san da cewa ba ga fannin da ya karanta ko ya karanto yake Farfesa ba. Don haka duk wani fanni da ke da alaƙa da fanninsa ta nesa da kusa ya ɗan kusance su ya ga ina aka kwana. Duk abin da ba ka fahimta ba ka kama bakinka ko da cikin fanninka yake bale na wajensa. A idon duniyar Farfesa ne da an ga kasawarsa wata magana sabuwa ke tashi shi ya sa gawurtattun 'yan wasan dambe da kokuwa da sharo in sun fita filin wasa ko mutuwa za a yi babu ja da baya. Dubi yadda makaɗa Muhammadu Nayawar ke yi wa ɗan dambensa Almu Ghana waƙa:

| | |
|---|---|
| Jagora: | Kai dai ban da gudu :Ko na gangara gebe na Ko da mutuwa za ta zo ta ɗauka<br>Ya sa maza laɓewa :Almu 'yan maza ka tsaro (Nayawar: 1976/72) |
| Yara: Gindi: | |

## Sakamakon Bincike

Farfesa kujera ce da a duniya jami'o'in ilmi ke bayar da ita. Wanda aka bai wa ita waɗanda suka bayar sun tabbatar da cancantar shi da kujerar a fannin da yake kai. Abin ban tsoro a yau ƙasarmu wasu jami'o'in Kudancin ƙasarmu sun fara saɓa wa wannan kujera ta saka siyasa a ciki wanda ya fara shafuwar Nijeriya ta Arewa. A haƙiƙanin gaskiyar ƙididdigar ma'aikatan Nijeriya a (2022) ya kai (720,000) idan an haɗa da na jihohi da ƙananan hukumomi bai kai (5,000,000) daga cikinsu a haƙiƙanin binciken adadi na Farfesoshin Nijeriya (10,000) kacal aka bar (4,500,000) da ba Furofesa ba. Ke nan a yau 2025 kowane Farfesa yana da gurbin ma'aikata (500) na Nijeriya amma ba ya da jallin ɗaukar nauyin da kansilan ƙaramar hukumarsu ke yi. Dukkanin ma'aikatan Nijeriya miliyan biyar ga malaman jami'a da Farfeoshi suka koyar suka samu ilmin zuwa aiki a biya su, kuma a ce sun fi Farfesoshin more wa a albashinsu an ya! Ba shakka Farfesoshi ke riƙe da ƙasa a ilmance da aikace domin in ba su babu ƙasar da ke iya awa ɗaya lafiya lau.

## Naɗewa

Buƙatun duniya ga Farfesa ita ce komai ya samu cikas su sa hannu da baki a gyara. Duk wani ci gaba da ake so a nemo su, su sa hannu a ci gaba. Su gyara matsalolin da aka gada da waɗanda ake ciki. A dubi ƙasashe wayayyi irin

su Masar a kowace ma'aikata ko wurin wani aiki na gwamnati sai Farfesa ake sa wa shugabantarsa wanda fannin karatunsa ya yi daidai da ma'aikatar. Yaushe za a sa Farfesan harshen Larabci jagoran kamfanin buga littattafan Larabci a ga kalmar innal Lahi ko innal Lahu ko innal Laahan? Da za a ba Farfesan tsaro shgabantar tsaron ƙasa za a ga bambancin rayuwa. A Nijeriya ta Arewa ya kamata a dinga sarrafa masana da masu ilmi jagorantar wuraren da ke da alaƙa da ƙwarewarsu. In har Gwamnatin Tarayya ba ta kula da albashin Farfesoshinta dubu goma kawai, to, ya kyautu a ce, da gwamnatin jiha da ƙaramar hukuma suna da hanyoyin da za su agazawa Farfesoshin yankinsu domin fuskantar matsalolinmu da gyara yankunanmu a ilmance.

**Manazarta**


Abdulƙadir, D. (1975) "The Role of an Oral Singer in Hausa/Fulani Society: A Case Study of Mamman Shata", PhD thesis, University of Indiana (Bloomington).

Bedu, A. M., Bashir, U. (2024). Generati*ve Approach to African Lingusitics and Literary Studies: A Festschrict in Honor of Professor Mohammed Munkaila*. Maiduguri: Faculty of Arts, University of Maiduguri Occassional Publication Series.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Fexe Al'ada. Lagos: Tiwal.

Bunza, A. M. (2009). *Narambaɗa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications.

Bunza, A. M. (2015). *In Ba Ka San Gari Ba Saurari Daka: Nazarin Muryar Mawaƙi Cikin Tafashen Gambu*. Egypt.

Bunza, A. M. (2024). Sannu ba ta hana zuwa ko za a daɗe ba a je ba (Farfesa Abdullahi Bayero Yahya a farfarjiyar Karatun Hausa) cikin Usman, B. B., Idris, Y., Sarkin Gulbi, A. da Abbas, N. I. (Editoc). *Ginshiƙin Nazarin Salon Waƙoƙin Hausa: A Festschrift in Honor of Professor Abadullahi Bayero Yahya*. Sokoto: Department of Nigerian Languages, UDUS.

Dawaki, A. M. (1974). "Alhaji Xanqwairo Maradun, Rayuwarsa da Waqoqinsa", Kundin digiri na farko (B.A.). Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S. M. (1996). Makaxa da Mawaqan Hausa. Kaduna: Fisbas Media Services.

Haliru, A. (1983). "Aliyu Ɗandawo da Waƙoƙinsa", Kundin digiri na farko (B.A.). Sokoto: Jami'ar Sokoto.

Mukhtar, I., Muhammad, A. S. da Lawal, N. (2025). *Kadarkon Adabin Hausa: A Festschrift in Honor of Professor Sa'idu Muhammad Gusau*. Kano: Department of Nigerian Languages, BUK.

Usman, B. B., Idris, Y., Sarkin Gulbi, A. da Abbas, N. I. (Editoci) (2024). *Ginshiƙin Nazarin Salon Waƙoƙin Hausa: A Festschrift in Honor of Professor Abadullahi Bayero Yahya*. Sokoto: Department of Nigerian Languages, UDUS.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a Rubuce: Tarihin Rubuce-rubuce cikin Hausa*. Zaria: NNPC.